*Yamtara-Wala Journal of Arts, Management and Social Sciences* (YaJAMSS)
Volume 2, Issue 1. December 2022 ISSN: 2971-5008

# AMFANI DA ADON HARSHE A WASU WAQOQIN ALHAJI (DR.) MAMMAN SHATA KATSINA

**Daga Saminu Sabo**
Department of Hausa, School of Languages,
College of Education and Legal Studies, Nguru,Yobe State.
08062563939, qibxau saminusabo3467@gmail.com

**TSAKURE**

A qasar Hausa kowane makaxi yana da salon yadda yake aiwatar da kixansa, kuma waxannan makaxan sukan bayar da gudummawa ta vangarori da dama. Saboda haka muradin wannan takarda shi ne fito da adon harshe a wasu waqoqin Alhaji Mamman Shata wanda suka haxa da: Kamantawa da Siffantawa da Jinsintarwa da Dabbantarwa da Abuntarwa da Alamtarwa da Kinaya da sauransu.Amma a wannan takardar mai taken amfani da adon harshe a wasu waqoqin Alhaji Mamman Shata a nan za a xauki uku daga ciki a yi bayani a kai kamar su: Kamantawa da Siffantawa da kuma Jinsintarwa ne. An xora wannan takardar ne a kan ra'in nazarin waqar baka Bahaushiya wadda Farfesa Sa'idu Muhammad Gusau ya samar a shekarar 1993. An yi amfani da Littatafai da takardu na ilimi da matanin waqar da kaset da kuma hira a matsayin hanyoyin da aka bi wajen gudanar da wannan binciken. Binciken ya gano nau'in adon harshe da Alhaji Mamman Shata yake amfani da su domin cim ma burinsa wajen nuna gwaninta da kuma iya sarrafa harshe a cikin wasu waqoqinsa. Har wa yau, binciken ya sake gano ta yin amfani da adon harshe ne makaxi zai saka waxansu kalmomi a xan waqa ba tare an fahimci saqonsa kai tsaye ba, dole sai an yi bayani.

**Kalmomin Fannu:** Amfani da Harshe da Waqa.

## 1.0 Gabatarwa

Alhaji Dr. Mamman Shata yana xaya daga cikin fittatun mawaqa a qasar Hausa.Ya yi waqoqi da dama a fannoni daban-daban da suka shafi rayuwar al'umma ta yau da kullum. Ba za a iya tantance iya waqoqin da Mamman Shata ya yi ba, don ya yi su da dama wasu akwai su a hannu wasu kuma babu su, kuma ba a san inda za a same su ba. Alhaji Dr. Mamman Shata ya bayar da gudummawa ta fuskar havaka harshen Hausa da adabi da al'adun Hausawa, har sai da ta kai Jami'ar Ahmadu Bello da ke zaria ta ba shi digirin girmamawa a fagen adabi a shekara ta 1988. Wannan maqalar ta duba wasu vangarori na adon harshe ne a wasu waqoqin Alhaji Dr. Mamman Shata. Don haka takardar ta qunshi taqaitaccen tarihinsa da asalin waqar baka da ma'anar waqar baka da ma'anar adon harshe wanda ya qunshi kamantawa da siffantawa da jinsintarwa da kinaya da alamtarwa da kuma qarangiya. Amma wannan takarda ta taqaita ne a kan kamantawa da siffantawa da kuma jinsintarwa.

## 1.1 Muradi

Babban muradin wannan takarda shi ne yin nazarin adon harshe a wasu waqoqin Alhaji Mamman Shata da ya rera da nufin fito da fasahar makaxin ta bayyana adon harshe a wasu waqoqin da ya rera.

## 1.2 Dabaru

An yi amfani da littafai da takardu na ilimi da matanin waqoqin makaxin da hira da kuma saurararan kaset a matsayin dabarun da aka yi amfani da su wajen gudanar da wannan binciken.

## 1.3 Ra'in Da Aka Xora Aikin A Kai

Ra'i shi ne hanyar nazari da wasu masana suka kafa ko suka bi don su riqa gudanar da ayyukansu ko nazarce-nazarcensu a kan

wasu sharuxxa ko ta amfani da salonsu don a gane su ko a bambance su daga wasunsu. Marcy (2001, :232)

Wannan aikin an xora shi ne a kan ra'in waqar baka Bahaushiya wadda Farfesa Sa'idu Muhammad Gusau ya samar a shekara 1993.

### 1.4 Taqaitaccen Tarihin Alhaji Dr. Mamman Shata Katsina

An haifi Alhaji Mamman Lawan Shata a unguwar Sanyinnawa cikin garin Musawa a Qasar Katsina a shekara ta 1923. Sunan mahaifinsa Alhaji Ibrahim Yaro. Sunan mahaifiyarsa Lariya. Mamman Shata bai tashi a cikin halin rashi ba. Shi xan gata ne ga asali da xinbin dangi. Shata ya girma a wajen iyayensa ba a kai shi riqo ba. Shata yana da alkunya, tun yana yaro yake da zazzaqar murya da fasaha a wajen waqe-waqensu na yara. Tun a shekarar 1928, lokacin da Mamman Shata ya cika shekara biyar da haihuwa, sai aka saka shi a makarantar allo a garin Musawa don ya sami ilimin addini kamar yadda aka saba saka Yara. Shata ya fara karatunsa a makarantar liman Xandauda da makarantar Malam Ali. Mamman Shata mutum ne mai himma, tare da neman na kai domin samun abin masarufi. A daidai shekara ta 1932 Shata ya fara tallace-tallacen kayan masarufi. Fitacciyar sana'ar da aka fi sanin Shata da ita, ita ce tallan goro, Shata ya yi tallan alewa kafin ya fara tallan goro. (Sheme 2006).

Mamman Shata ya sami laqabin sunan nan ne a lokacin da yake tallan goro. Idan an zo saye sai ya cika hannunsa da goron ya ba wanda ya zo saya maimakon ya bashi na daidai kuxin da za a saya. Daga nan ne ya sami laqabin 'Shata'. A wata faxar kuma wani xan'uwan Shata ne ya sa masa sunan Shata an ce wai idan ya sami kuxi ya kashe su idan Magaji ya tambaye shi ina kuxin? Sai ya ce "Na yi Shata da su". Wato na kashe. Daga nan sai ake kiransa da Shata kuma sunan ya bi shi (Sheme da wasu, 2006:43-59).

Sana'ar Mamman Shata ta xan hamsin ta jawo masa sanadiyar fara waqa, ta wannan hanya ce ya dinga bin kasuwanni don sayar da goro kuma a nan ne samari da 'yan mata sukan shirya wasan gargajiya a ranar kasuwa bayan an gama hidimar kasuwanci. A unguwar su Shata, saboda zaqin muryarsa sai aka zave shi da ya wakilce su. Shata shi yake zuwa na xaya saboda zaqin muryarsa duk lokacin ya yi waqa sai mutane suke sha'awar muryarsa. Daga nan aka sakar wa Shata har ake masa kirari Sarkin waqa. Wasu lokutan kuma akan zavi saurayi da budurwa su fito suna waqa da rawa, nan ma Shata shi yake yin nasara domin kaifin basirarsa. Haka zalika, Alhaji Mamman Shata ya shahara a wajen rera waqar " A sauwara" watau waqa ce da mawaqan baka suke fara yin ta kafin su zarce da gudanar da waqoqinsu. Mamman Shata shi ma ya yi tasa waqar ta kwaikwayon waqar A Sauwara. Ana rera waqar ne lokacin da aka zo wasan kwaikwayo tsakanin samari da 'yan mata.

Mamman Shata ya yi waqoqi da dama a fannoni daban-daban da suka shafi rayuwar al'umma ta yau da kullum. Mamman Shata ya yi waqoqi da dama da suka haxa da: waqoqin Yabo da na Koxa kai da na Tallace-tallace da na Faxakarwa da na zuga da na zambo da na siyasar kishin al'umma.

### 1.5 Asalin Waqar Baka

Daga cikin ra'ayoyin da masana suka bayar dangane da samuwar waqar baka sun haxa da: wasu suna ganin waqa ta samo tushe ne daga wajen wani maroqi 'Sasana'. Don haka masu wannan ra'ayin suna danganta makaxan Hausa da cewa jikokin wannan mutum ne da ake kira Sasana. Shi kuwa Sasana ya rayu ne a nahiyar Asiya. Daga bisani sai wasu daga cikin 'ya'yansa suka yiwo qaura zuwa qasashen Hausa.

Masu ra'ayi na biyu kuwa, suna ganin cewa, Hausawa sun sami waqa ne daga wajen tsofaffin daulolin Afrika ta yamma wato Ghana da Mali da Songhai. A wancan lokacin wai a daular Mali akwai su da

makaxan fada, kuma suna da alaqa ta kusa da makaxan Hausa, musamman ma makaxan fada. Masu Qauli na uku kuwa cewa suka yi, waqa ta samo hasken faruwa ne daga bautar iskoki ko dodanni. Hausawa a lokacin maguzanci sukan yi wa iskoki ko dodannin nan bikin cikar shekara ko kuma idan wani abu ya faru akan taru wajen abin bautar nan, su yi masa yanke-yanke da shaye-shaye. A wajen irin waxannan bukukuwa sukan yi wa abubuwan bautarsu zuga da kambamawa da hawar da su ta hanyar kirari ko kaxa take. Waqa ta ci gaba da bunqasa tun daga wancan lokacin har zuwa yau. (Abba da Zulyadaini 2000:)

### 1.6 Ma'anar Waqar Baka

Masana da dama sun tofa albarkacin bakinsu dangane da abin da waqar baka ta qunsa. Daga cikin waxannan masana akwai:

Sa'id, (1981:235) ya faxi cewa: " waqar baka ita ce wadda ake rerawa don jin daxi, a ajiye ta a ka, a kuma yaxa ta a baka."

Shi kuwa Gusau, (2003:xiii) cewa ya yi: "waqar baka Wani zance ne shiryayye cikin hikima da azanci da yake zuwa gava-gava bisa qa'idojin tsari da daidaitawa, a rera cikin sautin murya da amsa-amo na kari da kixa, sau da yawa kuma a tare da amshi."

A wajen Abba da Zulyadaini (2000:1) cewa suka yi "Waqar baka haxakar kalmomi da kixa ne cikin wani tsari mai bayar da armashi ga mai saurare, a inda shi mai sauraren zai iya tantance wannan haxaka ta kixa da jerin kalmomi".

Bisa waxannan ma'anoni da masana suka bayar a sama, dangane da yadda suka fahimci ma'anar waqar baka, a tawa fahimtar, ina ganin waqar baka magana ce da ake amfani da azanci wajen rera ta, tare da amfani da wasu sautuka na kixa ko waninsa wani lokaci har da taimakon 'yan amshi.

### 2.0 Ma'anar Adon Harshe

Kasancewar adon harshe shi ne batun da wannan takarda ta yi magana a kai na ga ya dace tun kafin aje ko'ina a fahimtar da mai sauraro ko karatu abin da waxannan kalmomi biyu suka qunsa. Masanin waqar baka, Gusau, (2003:54) ya bayyana waxannan kalmomi guda biyu da cewa: "Adon harshe wata dabara ce wadda ake yi wa harshen waqa kwalliya". Ya ci gaba da cewa a wajen adonta harshe akan zavo wasu kalmomi ne a zayyana waqa da su, a qawata ta sosai, ta yadda za a burge mai sauraro a kuma jawo hankalinsa. Akwai hanyoyi da yawa waxanda ake bi ta kansu a yi wa waqa ado. Ana buqatar mai nazarin waqa ya bibiyi waxannan abubuwa na adontawa da makaxi ya zuba su a cikin waqar da yake nazarin ya fito da su daki-daki. Daga cikin dabarun da ake amfani da su don yi wa waqoqi na baka ado akwai:

1. Kamantawa
2. Sifanatawa
3. Jinsintarwa
4. Kinaya
5. Alamtarwa
6. Karangiya

Sai dai kamar yadda aka bayyana a gabatarwa, takardar ta taqaita ne kawai ga kamantawa da siffantawa da kuma jinsintarwa.

### 3.0 Kamantawa

Kamantawa wata dabara ce wadda ake kwantata abubuwa biyu dangane da wasu darajoji da za su iya zama na daidaito ko na fifiko ko kuma na kashi. A lokacin da ake wannan za a yi amfani da wasu kalmomi da ke nuna kamanci a fili da ake kira kalmomin kamantawa ko kalmomi na tsakani, misali kamar: tamkar da awa da kama da sai ka ce da daidai da kaza da ca kake da wa da wace da zarce da tsere da xara da kasa da gaza da wane da babu kamar da bai kai da makamantan waxannan kalmomin da yawa. Kamantawa tana iya zama kamantawar daidaito ko kamantawar bambanto ko fifiko ko kuma kamantawar kashi ( A cikin Gusau :2003 :55). Ga misali

***Jagora:***
*:ina mamman waliyin Allah,*
*: Jikan waliyan Allah,*
*: Dattijo xan dattijo,*
*: Mai halin mutanen da can,*
*:Bai da halin mutanen yanzu,*
*:Ku yi magana da safe ku qulla,*
*:Yamma tai su ce sun fasa,*
*:Su mai da mutum kamar 'yan mata.*

***'yan amshi:***
*:Kwana lafiya mai Daura*
*:Jikan Abdu toron giwa,*

(Mamman Shata, Kwana lafiya )
A wannan xan waqar da ta gabata Mamman Shata ya kwatantan mutum da 'yan mata, kamar yadda ya ce mutanen da suke su an san su da magana xaya, kuma duk abin da za su yi, sukan yi shi ne bisa gaskiya da riqon amana. Amma mutanen yanzu ba su fiye yin magana xaya ba. Shi ya sa wasu in suna magana sai su ce kar ka min maganar 'yan mata . Kalmar kama a nan ita ce ta fito da kamancin a cikin wannan waqa.

Haka kuma akwai inda yake cewa:
***Jagora:***
*:Baba su mai da mutane kamar wasu mata,*
***yan amshi:***
*:Kwana lafiya mai Daura*
*:Jikan Abdu toron giwa.*

(Mamman Shata 'kwana lafiya)
Har ila yau kuma akwai inda yake cewa:
***Jagora:***
*:In na fara bakandamiya,*
*:Ji nike kamar malami gwanin tafsiri,*
*:Malamin amma fa gwanin tafsiri,*
*:A ja baqi ya fasa,*
*:Ba tare da jin tsoro ba.*
***'yan amshi:***
*:Alo-alo mai ganga ya gode,*
*:Yaran mai ganga sun gode.*

(Mamman Shata 'Bakandamiya)
To, a wannan xan waqar ma Mamman Shata ya kwatanta yadda yake kawo zubin kalmomi da fashin baqin rera waqa tamkar malami ne shi masanin fassara alqur'ani mai girma. To, a nan ma ya kwatanta kansa a matsayinsa na mawaqi da malami mai yin tafsiri a darajoji mabambanta na nuna gwaninta da azanci da naqaltar harshe a matsayin kwatance na daidaito.

### 3.1 Siffantawa

Gusau,(2003:57) Ya bayyana ma'anar siffantawa da cewa "Wata dabara ce inda makaxi yake xaukar siffar wani abu ya ba wa wani abu ba tare da amfani da wani tsakani ba".
Akwai misalan wasu waqoqin Alhaji Dr. Mamman Shata, inda yake nuna irin wannan siffantawa a cikin xiyan waqoqinsa kamar haka:
***Jagora*** :
*:Sardauna bahago Xan Hassan,*
*:Gulbi kar ka ci mai gardama,*
*:kogi kar ka ci mai gardama,*

***'Yan amshi:***
*:Sardauna bahago Xan Hassan,*
*:Gulbi kar ka ci mai gardama.*

(Mamman Shata, Waqar Sardauna Bahago Xan Hassan)
Idan muka duba a nan Mamman Shata ya yi amfani da dabara ta siffantawa, domin ya cim ma wani burinsa. Ma'ana ya siffanta Sardauna da cewa shi kogi ne, wanda bisa xabi'a kogi shi ne yake cinye mutum ko wani abu na ban tsoro. Amma ga shi Sardauna shi ne zai cinye mutane ba kogi ba. Har ila yau, makaxin ya sake amfani da irin wannan dabara ta siffantawa a wani xan waqar na daban kamar haka :
***Jagora:***
*:cuta dum maganarsa a nafsi take,*
*:Amadu shi maganar a nafsi take,*
*:Don ko mi ka ji yace maka,*
*:To ya tabbata za shi maka,*
*:Kai ko mi ka ji yai ma musu,*
*:To ya tabbata ba shi maka,*
*:Kutugun gamji magajin Hassan*

'***Yan Amshi:***
:*Sardauna Bahago Xan Hassan,*
:*Gulbi ka ka ci mai gardama.*

(Mamman Shata Waqar Sardauna Bahago Xan Hassan)
A waxannan xiya da suka gabata a xa na bakwai Shata ya siffanta Sardauna Amadu Bello da cewa shi kutungun gamji ne saboda alamar nagarta da juriya da qarko da Sardauna yake da ita wajen juriya da nagarta sai Shata ya siffanta shi da gamji. Idan aka lura da kyau a wannan xan waqar Shata ya yi la'akari da yadda gamji yake da juriya a cikin bishiyoyi wato dai duk abin da Sardauna yake yi yana son nuna wa jama'a ko al'umma mutum ya yi gaskiya don samun nasara a duk inda yake.
Har wa yau, kuma ya sake irin wannan dabarar ta siffantawa kamar haka:
***Jagora*** :
:*Bakin iya baqar fata kaf,*
:*Bakin riqon baqar fata kaf,*
:*Kai dumma mutumin da yake duniyar ga,*
:*Ko mai Hausa ko mara Hausa,*
:*Allah ko ya san gamji yana duniya.*

***'Yan amshi:***
**:***Sardauna Bahago Xan Hassan,*
:*Gulbi ka ka ci mai gardama.*

(Mamman Shata Waqar Sardauna Bahago Xan Hassan)
Bayan haka, wannan xan waqar ma Shata yana sake siffanta Sardauna da gamji duk mutanen Qasar Hausa da ma Turawa sun san Sardauna wajen gaskiya da kuma riqon amanarsa, wato Sardauna mutum ne wanda yake da juriya kamar na gamji wato dai duk wahala ko rintsi yana nan tare da gaskiyarsa.

### 3.2 Jinsintarwa

Yahaya (1995:6) cewa ya yi jinsintawa "Ana nufin a xauki wata siffa ta wani mutum a xora wa wani jinsi wanda ba mutum ba". Misali kamar yin magana da dabba ko tsuntsu ko qwaro da sauransu.
Xangambo (1981) cewa ya yi "Jinsintawa wata dabara ce wadda makaxi kan xauki wasu halaye ko siffofi ko darajoji da dai sauransu na wasu abubuwa da aka san bil Adama ne kaxai aka san shi da su, sai a laqaba wa wani abu marar rai. Ko dabba ko tsuntsu ko qwaro da dai sauransu".
Kalmar jinsi kalma ce mai nuna bambancin yanayi na halitta. Bayan jinsin mace da namiji akwai jinsin mutane da aljanu da dabbobi da qwari da tsuntsaye da bishiyoyi da duwatsu da ciyayi da sauransu. To, wannan makaxin yana amfani da irin wannan dabarar domin yana iya xaukar jinsin wani abu ya ba wa wani domin ya cim ma wani burinsa. Akwai wurare da dama da wannan makaxin ya yi amfani da wannan dabarar daga ciki akwai:
***Jagora*** :
:*Wata murna wurin Katsinawa,*
:*An ce Sani na hanyar nan,*
:*Sai tsalle suke, sai xouki,*
:*Cinnakan, bai san na gida,*
:*Har Shata yana duba wa.*

***'Yan amshi:***
:*Mai daga magajin mamman Sani Audi mai ban tsoro.*

(Mamman Shata Waqar Sani Audi)
Daxin daxawa, makaxin ya sake yin amfani da irin wannan dabarar ta jinsintarwa a wani wuri na daban. Duba wannan xan waqar mai zuwa:

***Jagora*** :
:*Sani gizago baka da sabo,*
:*Masassaqi ka tsare hannun ka,*
:*Kaifi namu Sani Audi.*

***'Yan amshi:***
:*Mai daga magajin mamman Sani Audi mai ban tsoro.*

(Mamman Shata Waqar Sani Audi)
Idan aka duba waxannan xiyan waqoqin da aka kawo na sama za a ga makaxin ya kira Sani Audi da Cinnaka wanda bai san na

gida ba, wato ba sani ba sabo ko nuna sanayya a harkokinsa na aiki da kuma zamantakewa ta yau da kullum. Domin idan har ana nuna sanayya to ba abin da zai tafi daidai a irin wannan rayuwar da ake gudanarwa. A xaya hannun kuma makaxin wannan waqar a wani xan waqar daban ya sake kiran Sani Audi da gizago baka da sabo, ma'ana dai duk yadda aka kai da sabo ga wani bai kai masassaqi da gizago, ba amma shi ma gizago yana iya yanka masassaqi a lokacin da yake amfani da shi wajen sassaqa. To shi ma Sani Audi haka yake duk wanda ya sani ya taka doka ko ya karya doka, to doka za ta taka shi duk girman sa duk mulkin sa da kuma matsayinsa.

## KAMMALAWA

Wannan takarda ta bayyana yadda makaxi Alhaji Mamman Shata Katsina ke amfani da adon harshe yayin rera waqoqinsa, tare da fito da irin fasahar da makaxin yake da ita a fannin adabin Hausa wajen iya amfani da gwanintar harshe. Sannan takardar ta gano adon harshe a wasu waqoqinsa da suka haxa da: Kamantawa da siffantawa da kuma Jinsintarwa kamar yadda yake a mazhabar Gusau, tare da qawata zancen da misalai daga waqoqin makaxi Alhaji mamman Shata. Ashe ke nan, takardar ta yi nazarin adon harshe ne a wasu waqoqin Alhaji Mamman Shata.

## MANAZARTA

Abba, M. da Zulyadaini, B.(2000). *Nazarin Kan Waqar Baka ta Hausa*. Zaria, Nigeria: Gaskiya Corporation Limited.

Bunza, A. M. (2009). *Narambaxa. Lagos*: Ibrash Islamic Communication Centre Ltd.

CNHN, (2006).*Qamusun Hausa*, Kano, Bayero University, Kano.

Xangambo, A. (1981). "*Xaurayar Gadon Fexe Waqa*". Takarda da aka gabatar a Taron Qara wa Juna Sani, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero: Kano

Gusau, S. M. (1996). *Makaxa da Mawaqan Hausa*. Kano: Benchmark Publishers Limited.

Gusau, S. M. (2002). *Salihu Jankixi Sarkin Taushi*. Kaduna: Baraka Press and Publishers Limited.

Gusau, S. M. (2003). *Jagoran Nazarin Waqar Baka. Kano*: Benchmark Publishers Limited.

Gusau, S. M. (2009). *Diwanin Waqoqin Baka. Kano*: Century Research and Publishing Limited.

Gusau, S. M. (2011). "Tarihi da Hanyar Nazarin Waqar Baka Bahaushiya a Taqaice"a cikin *Waqoqin Baka na Hausa.* Editoci; Funtua, A. I. da

Gusau, S. M. Katsina: Sashen Hausa, Kwalejin Ilimi ta Tarayyya.

Gusau, S. M. (2015). *Mazhabobin Ra'i da Tarke da Al'adu na Hausa*. Kano: Century Research and Publishing Limited.

Lawal, N. (2016). "Nazarin waqoqin Makaxan Bege na Hausa". Kundin Digiri na Biyu, Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano.

Satatima, I. G. (2009). "Waqoqin Xarsashin Zuciya na Makaxan Hausa" Kundin Digiri na Uku. Kano: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Sheme, I. da Wasu (2006) Shata Ikon Allah. Kaduna: Informat Publishers.

Sa'id, B. (1981). "Bambancin Waqar Baka da Rubutacciya". Takarda Cikin Littafin *Harshe, Adabi da Al'adu*: The Second Hausa International Conference, Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya. Kano: Jimi'ar Bayero.

Waxanda Aka Yi Hira da Su
Suna Mamuda Isa
Wuri Kasuwa Nguru
Lokaci 2.00pm
Ranar Alhamis

Kwanan Wata 7/09/2021
Suna Ibrahim Ali
Wuri Gidansa Bulabulin Ward Nguru
Lokaci 5.00pm
Ranar Asabar
Kwanan Wata 10/10/2021

Xan Asabe Isa
Wuri: Ofis, Kwalejin Ilimi Ta Garin Nguru.
Lokaci 2.00pm
Ranar Litinin
Kwanan Wata 18/10/2021